# *Rayuwar Ma'aurata*

*Hafiz Muhammad Sa'id*

Cibiyar Al'adun Musulunci

00989193544585 - 002348028403359

ISBN: .........................................

| | |
|---|---|
| Sunan Littafi: | Rayuwar Ma'aurata |
| Mawallafi: | Hafiz Muhammad Sa'id |
| Mai Yad'awa: | Cibiyar Al'adun Musulunci |
| Mai Bugawa: | Jami'atul Mustafa |
| Bugu: | Na Farko, 1431, 2010, 1389 |
| Adadi: | 1000 |
| Email: | hfazah@yahoo.com |


Ba a yarda wani ya buga wannan littafi ba

بسم الله الرحمن الرحيم

*Godiya ta tabbata ga Allah (s.w.t) Kuma Aminci ya k'ara tabbata ga bayinsa wad'anda ya zab'a*

*Kuma akwai daga ayoyinsa, ya halitta muku matan aure daga kawukanku, domin ku nutsu zuwa gareta, kuma ya sanya soyayya da rahama a tsakaninku, lalle a cikin wannan akwai ayoyi ga mutane masu yin tunani*[1].

[1] Surar Rum: 21.

## Gabatarwar Mai Yaxawa

"Su tufafi ne gareku, kuma ku tufafi ne garesu". Baqara: 187.

Mutum halitta ne na al'umma da zaman cikin iyali wanda yake shi ne mafi qarancin haxuwar zaman tare, amma a lokaci guda kuma mafi zama asasin gina al'umma, wanda wannan asasin an gina shi ne da namij da mace. Sanin nauyin da ya hau kan namiji da mace, da sanin yanayi da ayyuka da alaqar yadda za a zauna da juna tsakanin namiji da mace shi ne abin da yake iya qarfafa danqon soyayya mai qarfi da alaqa tsakanin iyali.

Kuma kai mutum! Shin ka san kuwa wajibi ne a kanka ka xaukaka himmarka zuwa ga Allah (s.w.t) domin kai ba a yi ka don ka xamfaru da duniya mai turvaya ba, "Ina zaku ne"[1]. Shin kuwa ka san cewa kana da wani nauyi da ya hau kanka?

[1] Takwir: 26.

"Ku kare kawukanku da iyalanku daga wuta, wacce gumagumanta su ne mutane da duwatsu"[1].

Wannan littafin da yake gabanku an rubuta shi ne da qoqari da himmar mai girma Hafiz Muhammad Sa'id, kuma vangaren tarjama da yaxa littattafai na Jami'ar Mustafa ne ya yaxa shi domin gabatarwa ga masu magana da harshen Hausa, tare da girmamawa ga mawallafin.

[1] Tahrim: 6.